# Dokar Jinsi ta Ƙasa (NGP) A saukake 2021-2026

WRAPA

MacArthur Foundation

FEDERAL MINISTRY OF WOMEN AFFAIRS

# Dokar Jinsi ta Ƙasa (NGP) A sauƙaƙe

## 2021-2026



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

**DOKAR JINSI TA ƘASA (NGP) A SAUƘAƘE**
**2021-2026**

Haƙƙin mallaka © (WRAPA)
An Wallafa a Nijeriya a shekarar
2023

Ba a yarda a sake samar da wani ɓangare na wannan wallafa, wanda da za a iya sake samarwa, ko a adana a cikin wani tsari na ajiya ko aikawa ta kowane tsari ko ta kowace hanya a kwamfuta ko inji ko a kwafa ko a naɗa ko wani abu, ba tare da rubutaccen izinin mai wallafa kafin yin hakan ba; sai dai don ɗan yanko zance a jarida ko mujalla ko bitar littafi ko don amfanin da ba na kasuwanci ba, wanda dokar haƙƙin mallaka ta ba da izini.

ISBN: 978-978-780-610-4



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# ABUBUWAN DA KE CIKI


| | |
|---|---|
| GODIYA | v |
| SHIMFIƊA | vi |
| GABATARWA | vii |
| SHARE FAGE | viii - x |
| SAƘANDAMAI | xi - xii |
| ME YA SA AKE BUKATAR DOKAR JINSI? | Shafi na 1 |
| ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA ƊAYA: TSARIN SAMAR DA DOKA DA DOKA | Shafi na 2 |




*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA BIYU: INGANTA TATTALIN ARZIKI DA KWAZO DA RAYUWA — Shafi na 4

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA UKU: BUNKASA ƊAN'ADAM — Shafi na 12

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA HUƊU: GEESI A WASU MUHIMMAN CIBIYOYIN ƁANGARORIN ZAMANTAKEWA — Shafi na 26

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA BIYAR: GEESI A ƁANGAREN TSARO — Shafi na 34

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA SHIDA: GEESI A DAMAR SAMUN ADALCI DA HAƘƘOƘIN ƊAN'ADAM DA SHUGABANCI — Shafi na 41

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA BAKWAI: GEESI DA JAGORANCI DA SHIGA SIYASA — Shafi na 47

ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA TAKWAS: GEESI DA ƊABI'UN JINSI DA GUDANAR DA AL'ADUN ZAMANTAKEWA — Shafi na 53




*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*
MacArthur Foundation

# Godiya

Ana cewa wanda za shi sama idan ya taka ƙeda ma ya rage tafiya. Yunƙurin samar da Dokar Jinsi ta Kasa A Sauƙaƙe (NGP) 2021 - 2025 ya fara ne da ƙwaƙƙwaran tallafi da himmar Gwamnatin Nigeriya, na ta haɓaka daidaiton jinsi da inganta haƙƙoƙin mata. Sadaukarwar da gwamnatin Nijeriya ta yi a wannan fafutika shi ne ya zama ɗan ba wajen samarwa da aiwatar da Dokar Jinsi ta Kasa.

Kungiyar WRAPA tana miƙa godiyarta ga Ma'aikatar Harkokin Mata ta Tarayya kuma musamman ga Maigirma Ministan Harkokin Mata, Dame Pauline Tallen, CON, OFR, KSG, saboda kyakkyawan jagorancinta. Shawarwari da ƙwarewar jagorancin Sashen Jinsi ta hanyar bitar Dokar Jinsi ta Kasa ya zama wani sinadari na samar da wani daftari da ya zama sassauƙa. Kyakkyawar fahintar da suka yi wa al'amuran da suka shafi jinsi ya mayar da haɗin guiwar tsakanin WRAPA da Ma'aikatar Harkokin Mata don samar da Dokar Jinsi ta Kasa, wani haɗin guiwa mai tsari kuma mai aiki.

Kungiyar WRAPA tana godiya da tallafi da haɗin kan Gidauniyar MacArthur a Nijeriya, bisa yarda da ƙaramar fikira ta sauƙaƙa sabuwar dokar. Tallafin kuɗinsu da nusarwarsu sun zama sinadaran da suka ba da damar sarrafa yunƙurin masu ruwa da tsaki yadda ya kamata ta wajen yaɗawa da sauƙaƙa daftarin doka mai sarƙaƙiya don inganta shigar da kowane jinsi da kuma ɗaukar nauyi. Dole mu ambaci Dr. Amina Salihu, Mataimakiyar Darakta a Gidauniyar MacArthur, saboda sa idanunta da tallafinta a gaba ɗaya aikin samar da Dokar Jinsi ta Kasa.

Haka kuma muna miƙa godiya da yabawa ga rukunin ƙwararrun Dokar Jinsi ta Kasa, masu sadaukar da kai, a ƙarƙashin jagorancin Farfesa Olabisi Aina, wanda ya nuna ƙwarewa da sha'awa da aiki tuƙuru ba dare ba rana don gyara bayanai da tsarin Dokar Jinsi ta Kasa A Sauƙaƙe. Haka kuma aikin sauƙaƙa dokar ya amfana da ƙwarewar Antinuke Odukoya da Temitope Banso da Amina Alhassan da Victor Ibim Boma.

Ba za mu manta da gudummawar mambobin shirin Tallafin WRAPA da MacArthur wajen Inganta Mutunta Zaɓe da Ɗaukar Nauyi wato (IEIA) da Hukumar Tallafa wa Mata (NWTF) da Cibiyar Bincike da Adana Bayanai a kan Kare Haƙƙoƙin Mata (WARDC) da Zauren Mata a Siyasa, (WiPF) da Rukunin Mata 100 da ƙungiyar Mu Zaɓe Ta da ƙungiyar Rajin Kawar da Cin Zarafi ga Mata (NCCA) da GERCON, da the Ɓangaren Kwararru a JInsi (GTU). Akwai kuma rawar a yaba da Shirin IEIA Abokan Hulɗar NGP a matakin jiha, da Cibiyar Cigaban Albarkatun Fararen Hula da Adana Bayanai (CIRDDOC) da ƙungiyar YaƊa Manufa a Nijeriya da Cibiyar Bincike da Adana Bayanai ta Kebetkache da Cibiyar Sadarwa ta Matan Kasa da Kasa (IWCC) suka taka duk a wajen yaɗa sabuwar Dokar Jinsi a matakin farko.

Muna godiya da yaba wa gudummawar ma'aikatan WRAPA wajen aikin sauƙaƙa Dokar Jinsi ta Kasa, musamman rukunin aiwatar da shirin IEIA. Muna yabawa da shawarwari da jagorancin rukunin ƙwararru a ƙarƙashin jagorancin Wumi Asubiaro Dada, wadda Anisah Ari da Oluwayemisi Nathaniel da Zainab Abdurasheed da Paul Adama da Habiba Ahmed da Jovita Chehchet da Shafi'u Barde suke dafa mata. Sadaukarwa da haɗin kan rukunin ya zama mai muhimmanci wajen samun nasarar aikin sauƙaƙa dokar.

Daga ƙarshe Kungiyar WRAPA, za ta so ta miƙa godiyarta ga dukkan waɗanda suka ba da gudummawa wajen samar da Dokar Jinsi ta Kasa A Sauƙaƙe 2021 - 2025 a matsayin wani kayan aiki na sauya al'umar Nijeriya zuwa al'ummar da take mutuntawa da riƙo da haƙƙoki da mutuncin kowa.

Saudatu Mahdi MFR
Babbar Sakatariya
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata (WRAPA)

# Shimfiɗa

Gidauniyar MacArthur A kan Shirin Nijeriya tana farin cikin tallafa wa Dokar Jinsi ta Kasa ta Nijeriya, 2023. Mun bibiyi aikin sake duba dokar ta hanyar tallafin mambobin ƙungiyar ƙwararrunmu ga Ma'aikatar Harkokin Mata ta Tarayya. Haka kuma mun yi farin ciki da hangen nesa da kuma ƙarfin guiwar abokan hulɗarmu, wato Kungiyar Kare Haƙƙokin Mata WRAPA, da ta kawo tsarin haɗin guiwar yaɗawa da wayar da kai don tabbatar da an yayata an kuma fahimci dokar jinsi kuma masu ruwa da tsaki na ciki da waje sun aiwatar da ita.

Mafi muhimmanci a Shirin Nijeriya shi ne yadda sanya hannun jarinmu ya haɓaka ingancin rayuwar mutanen da suke fama da talauci. Mun sani daga bayanan da suka gabata da kuma kallon abin da yake a zahiri cewa sanya ɗan hannun jari wajen inganta rayuwar mata da 'yan mata zai iya kawo gagarumin sauyi a dukkan rayuwar al'umma. Sanya hannun jari a kan mata yana kawar da gibin da ake da shi ta fannin jinsi kuma ya amfani tattalin arziki da al'umma.

Doka jerin ƙa'idoji ne da dokokin da suke bayyana inda aiki zai sa gaba don inganta rayuwar 'yan ƙasa. A irin wannan yanayi, 'yan ƙasa talakawa da ba sa cikin, ko da suke bakin iko sun rasa samun dama a dalilin jinsinsu da wayewarsu. Abin baƙin ciki, mafi yawan waɗannan mutane mata ne da 'yammata. Don haka, sai aka samar da salon magana na cewa 'talauci na mata ne' saboda talauci yana ɗauke da fuskar mata, tun da a cikin duk talaka 4, akwai yiwuwar 3 su zama mata ne mabuƙata. Sanya hannun jari don wayar da kan mutane a kan dokar jinsi ta ƙasa da aka yi wa kyakkyawan tsari, abu ne da ya cancanta don a tabbatar da cewa masu ruwa da tsaki, waɗanda suka haɗar da mata da al'ummominsu, sun sami ayyuka masu inganci da kuma sakamako mai daidaito da damammakin da suka kamace su.

Duk da yake ƙuduri ko kuma ma doka wajibi ne amma sun yi kaɗan su samar da sauyi, sai dai za su iya ba mu dama mu fara bin wani tafarkin sanya hannun jarin da ya dace. Za su ba mu dama mu fahinci manufar gwamnati ko kuma mu kama su da laifi. Duk da haka, idan ana son dokar ta yi aiki, dole waɗanda za su amfana su zama suna sa ido a kan imanin masu yin doka a dukkanin dokoki. A wannan lamari, ba wai kawai mata da 'yammata ba, a'a, dole dukkanin masu ƙaunar adalci da samun daidaito su yi tambayar, yaya ingancin yadda ake aiwatar da dokar jinsi ta ƙasa? Yaya ake ɗabbaƙa ta a matakin jiha? Waɗanne sakamako muke gani kuma muke fatan tabbatar da su? Wane gibi ne ya saura ba a cike shi ba?

Akwai wasu abubuwa da suke na gida da wannan dokar jinsin ta ƙasa take da su da suka cancanci a ambace su. Na farko an yi mata lokaci 2021-2026, wanda hakan yake nuna cewa akwai buƙatar a ci gaba da sauya dokar a kuma tabbatar da ana kallon lokuta na damar bibiya da aka buɗe na shekara 4, ta haka za a tabbatar da cewa ana shigar da sababbin al'amura da suke tasowa, ta yanayin da zai tabbatar da dacewarsu wajen gyara dokar. Wataƙila ma kauce wa jinkirin shekara 16 na sake bitar dokar shekara ta 2006, wadda sai a shekara ta 2022 kawai aka yi bitar ta.

Wani abu mai muhimmanci shi ne samar da matsayin Ma'aikatar Harkokin Mata ta Tarayya (MWA) a matsayin mai samar da kayan aiki don samar da daidaiton jisin a dukkan ma'aikatu da sassa da hukumomi, su nemi samar da daidaiton jinsi da tafiya tare da kowa, kuma ba ma'aikatar mata ce za ta riƙa aiki ita kaɗai ba. Ma'aikatar Harkokin Mata tana da muhimmanci, ba wai kawai don ita alama ce ta nuna himmar Nijeriya ga daidaiton jinsi da tafiya da kowa ba, sai dai don cewa tana zama wata shaida ta irin fahimtar da Nijeriya ta kawo a matsayin ƙasar da a gaske ta himmatu ta ga ta daidaita yanayin aiwatarwa da kawar da wariya da nuna bambanci da takurawa. Dole mu tuna da gargaɗin UNDP na cewa cigaban da ba jinsi barazana ne.

Abu na uku da aka samar shi ne tsarin sadarwa da aka saka shi a cikin Dokar Jinsi ta Kasa don a samar da ita ga al'ummomi daban-daban a cikin sassauƙan Ingilishi tare da hotuna, wanda kuma ma za a samar da ita a cikin wasu harsunan gida. Wannan wani kyakkyawan ɗan ba ne na mallakar Dokar Jinsi ta Kasa, wadda muke buƙatar gwadawa mu kuma miƙa kyawawan dokoki gaba.

Kole Ahmed Shettima
Editan Afrika
The John D, and Catherine T. Gidauniyar MacArthur
Abuja

# Share Fage

Yayin da muke wani buki mai matuƙar tarihi, wanda mafarki ne ya zama gaske: Wato ƙaddamar da Sabuwar Dokar Jinsi ta Ƙasa - NGP ta shekarar 2021 zuwa 2026, zan so na yaba wa Maigirma Shugaban Ƙasa Muhammadu Buhari, GCFR bisa tallafinsa da tabbatar da samar da wannan doka. Rawar da abokan aikina suka taka na amincewar dukkan mambobin Majalisar Zartarwa ta Ƙasa, wata shaida ce ta nuna himmar sanya maganar jinsi a kowane ɓangare na Cigaban Nijeriya.

Zan so na yaba wa jagorori a cikin wannan ɗan ba da aka saka, bisa himma da tallafin Bankin Cigaban Afrika (ADB) da Gidauniyar MacArthur da dukkan sauran abokan hulɗa masu bayar da tallafin cigaba. Gudummawarsu ta zama wani muhimmin matakin da ya taimaka wajen cimma daidaiton jinsi sannan kuma da inganta rawuyar ɗaiɗaikun mutane, ba tare da la'akari da jinsi ba, don tabbatar da muhimmancinsu.

Shekara da shekaru mun yi ta ƙoƙarin samar da al'umma, wadda kowanne ɗan ƙasa zai iya yin ƙoƙarinsa ba tare da la'akari da jinsinsa ba. Duk da cewa mun sami cigaba, amma mun gano cewa har yanzu akwai aiki ja a gabanmu. Sabuwar Dokar Jinsi ta Ƙasa (NGP), a matsayinta na kayan aiki, za ta ɗora a kan wannan, don ta jagorance mu zuwa ga ƙarin shigar da kowa da daidaito da kuma rayuwar adalci nan gaba, ba tare da barin kowa a baya ba. Dokar ta yi la'akari da muhimmancin shigar da maza manya da yara a matsayin abokan ƙawance a tafarkin samar da daidaiton jinsi. Dokar ta magance matsalolin masu sarƙaƙaya da mata da 'yammatanmu suke fuskanta. Dokar ta ƙarfafa buƙatar da ake da ita na kawar da duk wani nau'in nuna wariya da tashin hankali da abubuwan cutarwa ga mata da 'yammata kuma dokar ta fito da muhimmancin samar da dama baiɗaya ta samun ingantaccen ilimi da kula da lafiya da damammakin tattalin arziki ga kowa. Haka kuma ta haɓaka shigar mata a dama da su a wajen yanke hukunci, tana mai kula da muhimmiyar gudummawarsu ga jagoranci da samar da dokoki.

A yayin da muke rungumar wannan doka da kuma kira a kan aiwatar da ita, dole mu tuna cewa, cimma daidaiton jinsi na gaskiya yana buƙatar gudummawar kowa. Wannan shi ya jawo kira ga haɗin guiwa tsakanin gwamnati da ƙungiyoyin fararen hula da masu zaman kansu da masu ba da tallafi da al'umomin da suka ci gaba; da su ci gaba da haɓaka daidaiton jinsi a wuraren aikinmu da makarantunmu da cikin al'umarmu. Ina kira ga masu ɗauke da nauye-nauye a Ma'aikatu da Sassa da Hukumomi da iyalai da masu ruwa da tsaki a cikin al'umma da 'yan ƙasa baki ɗaya, da su yi amfani da wannan kwafi don su saba da Sabuwar Dokar, su kuma riƙe ta a matsayin tasu, su kuma tallafa wa kiran da ake yi na aiwatar da ita.

Ina yaba wa Kungiyar Tallafa wa Mata (WRAPA) da dukkan waɗanda suka yi aiki tuƙuru wajen samar da wannan sassauƙa, bayyanannen samfurin dokar kuma mai duban gaba. Sadaukar da kanku wajen haɓaka daidaiton jinsi da adalci a tsakanin al'umma abin ƙarfafa guiwa ne. 'Yan Nijeriya suna zuba ido don ganin fassarar wannan sassauƙan samfuri a cikin wasu daga cikin harsunan Nijeriya, don a saukar da faɗakarwar zuwa ƙasa, a ɗauke ta a kuma nemi aiwatar da Sabuwar Dokar Jinsi ta Kasa - NGP ta shekarar 2021 zuwa 2026.

Dame Pauline K. Tallen, CON, OFR, KSG
Maigirma Ministar Harkokin Mata
2023

# Gabatarwa

Dokar jinsi ta shekarar 2021 ta fahimci cewa mata suna fuskantar tarnaƙi wajen cimma samun cikakken daidaito da ingancin rayuwa da ci gaba saboda Shugabantar da maza da tsarin wayewa da nakasa da matsayin tattalin arzikin zamantakewa haɗi da yanayin rayuwarsu - 'yan gudun hijira daga birane ko karkara a sanadiyyar bala'o'in muhalli da nau'o'in tashin hankali daban-daban (ayyukan ta'addanci da satar mutane da fashin daji) da annoba. Ma'aikatar Harkokin Mata ta Tarayya (FMWA) bisa nauyin da ke kanta tana yunƙurin tabbatar da tabbataccen cigaba mai ɗorewa na mata da mazan Nijeriya ta hanyar samar da tsarin haɓaka cigaban ƙasa, wanda zai tabbatar da rayuwa da kariya da cigaba da shigar kowa a dama da shi, musamman waɗanda bisa al'ada suke cikin ajandar cigaban ƙasa.

Rukunin da aka nufa na asali, su ne mata da ƙananan yara da tsofaffi da masu buƙata ta musamman da masu neman kariyar a zamantakewa da rashin adalcin zamantakewar da nuna wariya.

Dokar Jinsi ta Kasa ta shekarar 2006 ta taimaka ta hanyoyi da dama. Ta taimaka musamman ta jan hankalin mutane zuwa ga haƙƙoƙin mata da 'yammata da sauran rukunin masu fuskantar haɗari a cikin al'umma. Aiwatar da tanade-tanaden dokar sama-sama, duk da himmar da gwamnati ta nuna, ya sa an nemi a yi kiran faɗakarwa don ƙara ɗaukar mataki daga wajen masu ruwa da tsaki. Wannan yana da muhimmanci saboda a duk al'amura na musamman da suke shafar rayuwar mata, kamar inganta tattalin arzikin rayuwa da ilimi da kula da lafiya da ababen more rayuwa na zamantakewa da shiga a dama da su da samun damar kujerun shugabanci da jagoranci, ana sa su ne a mataki na biyu.

Saboda haka, sake bitar Dokar Jinsi ta shekarar 2006 ya zama dole saboda waɗannan:

i. Duk da cewa mata su ne kimanin rabin yawan mutane, kuma su ne kimanin kaso 60 cikin ɗari na masu yin zaɓe a Nigeriya (UN Women, 2019), amma har yanzu akwai giɓin jinsi ta ɓangaren wakilci a wajen yanke hukunci, samun dama da kula da albarkatu da damammakin tattalin arzikin zamantakewa;

ii. Saukar ƙwazon tattalin arziki da talauci da taɓarɓarewar al'adu na gari da matsalar tattalin arzikin duniya sun ƙara haɗari ga talakawa da waɗanda ake dannewa da zawarawa da masu buƙata ta musamman da marayu da musamman mata da 'yammata;

iii. Buƙatar yin aiki sau da ƙafa da tsarin yin bita na lokaci-lokaci, a matsayin wani mataki da aka ɗauka a cikin dokar, na bibiyar dokar da ƙwazon aiwatar da tsari da auna cigaba da darussan da aka koya da kuma rungumar batutuwa masu tasowa;

iv. Ma'aunan asali da na ƙwazo sun bayyana cewa akwai wawakeken giɓin jinsi a Nijeriya idan aka kwatanta da wasu ƙasashen, hakan sai ya ba da dama a yi jan hankali a kan lokaci a kan batutuwa masu muhimmanci;

v. Batutuwan jinsi da suke tasowa da yanayin Muradun Cigaba Mai Ɗorewa, waɗanda suke buƙatar doka da manufofin da aka tsara su don su cimma sabon matsayin da aka aminta da shi a duniya, da ma wasu abubuwan;

Zuwa yanzu, Ma'aikatar Harkokin Mata ta Tarayya da haɗin guiwar WRAPA da sauran Kungiyoyin fararen hula sun yi aiki don su tabbatar da cikakkiyar bita da aikin tantancewa a shekarar 2021; suka tattaro bayanai da gudummawa daban-daban daga dukkanin abokan haɗin guiwa. Amincewa da sabuwar Dokar Jinsi ta Kasa da Majalisar Zartarwa ta yi a watan Maris 2022 wani mataki ne da ya share hanyar aiwatar da ita. An gudanar da tattaunawa daban-daban da ta danganci muhimman ɓangarorin mulki, waɗanda suka haɗar da hukumomi da sassan gwamnati da jami'an tsaro da Hukumar zaɓe da ɓangaren jarida da shuwagabannin al'ada da na addini, don a samar da wani yanayi na tunkarar fara aiki da kuma aiwatar da dokar ta kowane ɓangare.

Haka kuma a halin yanzu ana kan gudanar da tallace-tallacen yaɗawa, ta gidajen rediyo da na talabijin da kafofin sada zumunta don yaɗa sabuwar dokar jinsin. Sabuwar dokar ta kai ta iya mayar da batun jinsi ya zama al'ada da kuma buƙatar da ake da ita na wuraren aikin gwamnati da makarantu da ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba da ƙungiyoyin addini da na al'ada da dukkanin ɓangarorin mulki a gwamnatance da su rungumi adalcin jinsi. Buƙatar a daidaita maganar jinsi a dukkanin ɓangarorin gwamnati ba ƙaramar aba ba ce, kamar yadda Shugaban Kasa Muhammadu Buhari CGFR ya faɗa a kalamansa:

> ***"Nuna wariya ga mata da 'yammata a ma'aikatun gwamnati da na masu zaman kansu yana ci gaba da jan hankalinmu. Ya kamata a sami cikakken wakilcin mata da maza, yara da 'yammata da waɗanda ake warewa a zamantakewa a cikin gwamnati da ma kowane bangare na mu'amala, don a ba su dama su cimma muradunsu."***

Haka kuma buƙatar samun yunƙuri da haɗin guiwa tsayayye don cimma tanade-tanadenta sun bayyana a fili a bayanan Maigirma **Ministar Harkokin Mata - Dame Pouline Tallen, CON,OFRKSG:**

> ***A tsakiyar aiwatar da Dokar, akwai buƙatar yanayin da zai iya, mai kai ɗauki kuma mai ɗaukar nauyi da kuma sa idanun ƙungiyoyin fararen hula.***

Don haka, WRAPA da sauran ƙungiyoyin mata waɗanda ba na gwamnati ba da tallafin Gidauniyar MacArthur suka gano buƙatar sauƙaƙa samfurin sabuwar Dokar, a matsayin wata hanya ta tabbatar da cikakkiyar fahimtar tanade-tanadenta don kowanne ɗan ƙasa ya fara aiki da ita da kuma kira ga dukkanin masu ruwa da tsaki su shiga a dama da su a wannan yunƙuri na tabbatar da aiwatar da sabon samfurin dokar don cigaba baki ɗaya.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

## SAƘANDAMAI

**AfCFTA:** Yankin Ciniki Kyauta na Nahiyar Afrika

**AIDS:** Cutar Ƙanjamau

**CBOs:** Ƙungiyoyin Fararen Hula

**CEDAW:** Taron Kawar da Duk Wani Nau'in Nuna Wariya ga Mata

**COVID-19**: Cutar Korona ta 2019

**CSOs:** Ƙungiyoyin Fararen Hula

**CSR:** Tsarin Kasuwanci Mai Kula Da Al'umma

**EFCC:** Hukumar Hana yi wa Tattalin Arzikin Ƙasa Zagon-ƙasa

**EWER:** Gargaɗi a Kan Kari da Kai Ɗauki a Kan Kari

**GBV:** Nuna Rashin Imani Dangane da Jinsi

**GEESI:** Daidaiton Jinsi da Inganta Rayuwar Mata da Shigar da Kowa a Zamantakewa.

**HIV:** Ƙwayar Cutar Ƙanjamau

**ICPC:** Hukumar Hana Cin Hanci da Rashawa

**ICT:** Fasahar Sadarwa

**IDPs:** Mutanen da aka Tilasta wa Gudun Hijira

**INEC:** Hukumar Zaɓe ta Ƙasa

**INGOs:** Ƙungiyoyin Ƙasa da Ƙasa da ba na Gwamnati ba

**LGA:** Yankin Ƙaramar Hukuma

MDAs: Ma'aikatu da Hukumomin Gwamnati

**MSMEs:** Ma'aikatar Ƙanana da Matsakaitun Masana'antu

**NAFDAC**: Hukumar Kula da Abinci da Magunguna ta Ƙasa

**NBTE:** Hukumar Kula da Ilimin Fasaha

**NEMA:** Hukumar Agajin Gaggawa ta Ƙasa

**NGO:** Ƙungiyar da ba ta Gwamnati ba

**NGOs:** Ƙungiyoyin da ba na Gwamnati ba

**NGP:** Dokar Jinsi ta Ƙasa

**NOA:** Hukumar Wayar da Kai ta Ƙasa

**NUC:** Hukumar Kula da Jami'o'i ta Ƙasa

**PLWHA:** Mutanen da Suke Ɗauke da Cutar Ƙanjamau

**PWD:** Mai Buƙata ta Musamman

**PWDs:** Masu Buƙatu na Musamman

**S/GBV:** Nuna Rashin Imani Dangane da Jima'i ko Jinsi

**SEMA:** Hukumar Agajin Gaggawa ta Jiha

**SGBV:** Nuna Rashin Imani Dangane da Jima'i da Jinsi

**SURE-P:** Shirin Juya Kuɗi Cikin Sauƙi da Inganta Rayuwa

**UNHCR:** Hukumar Kula da 'Yan Gudun Hijira ta Majalisar Ɗinkin Duniya

**UNSCR:** Kwamitin Tsaro na Majalisar Ɗinkin Duniya

**VAPP:** Hana Nuna Rashin Imani ga Mutane

**VAW:** Nuna Rashin Imani ga Mata

**WASH:** Ruwa da Tsaftar Muhalli da ta Jiki

# Me Ya Sa ake Buƙatar Dokar Jinsi?

An tsara Dokar Jinsi ta Ƙasa ne da manufar bunƙasa Daidaiton Jinsi da Inganta Rayuwar Mata da Shigar da Kowa a Zamantakewa a dukkan manufofi da shirye-shirye a ɓangaren gwamnati da masu zaman kansu a Nijeriya. Haka zai sa Nijeriya ta zama al'ummar da mata da maza da 'yammata da yara suke more damammaki da haƙƙoƙi da nauye-nauye iri ɗaya.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation


## ƁANGAREN DA AKA BA FIFIKO NA ƊAYA:
# TSARIN SAMAR DA DOKA DA DOKA

## Halin da ake Ciki:

1. Kundin Tsarin Mulkin shekara ta 1999 (kamar yadda aka yi masa gyara) bai ba da haƙƙi daidai ga mata da maza ba.



2. Akwai dokokin nuna wariya a ɓangarorin gwamnati da masu zaman kansu.



4. An zartar da dokar Hana Nuna Rashin Imani ga Mutane (VAPP) ta shekarar 2015 a kimanin Jihohi 34, amma har yanzu ana samun ƙaruwar nuna rashin imani da ya danganci jinsi ko jima'i.





*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

## Matakan da ake Bukatar Dauka:

1. A goya wa matakin tabbatar da tsarin 50:50 baya a Nijeriya, a wajen nadin mukami da kujeru zababbu.
2. A goya wa aiki da tanade-tanaden CEDAW a kotuna baya.
3. A yi aiki da nuna damuwa da jinsi a matsayin wani tsari na cigaba a kowane bangare.
4. A horar da ma'aikatan gwamnati da masu zaman kansu a wajen amfani da tsarin aiki da yake la'akari da dukkan jinsi da kuma ka'idojin kasafin kudi da zai yi wa kowa daidai.
5. A kara sanya hannun jari wajen horar da mata a kan jagoranci a mukamai.
6. A ba da sakamako ga yin aiki da dokoki da manufofin da suka danaganci jinsi a kuma yi hukunci ga kin yin aiki da su.
7. A horar da ma'aikatan shari'a da hukumomin dabbaka doka a kan tsarin shari'a mai daukar mataki kai tsaye a kan harkokin jinsi.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a dukkan matakai.

Al'umma bakidaya.

Abokan kawo cigaba.

Ma'aikatar Harkokin Mata da sauran Hukumomin Gwamnati.

Kungiyoyin Yada Manufa da da sauran kungiyoyin fararen hula.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Hakkin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# ƁANGAREN DA AKA BA FIFIKO NA BIYU:

# INGANTA TATTALIN ARZIƘI DA ƘWAZO DA RAYUWA

## (A). Aikin Gona da Raya Karkara

### Halin da ake Ciki:

- Mata su ne kimanin kaso **60 cikin ɗari** na ma'aikatan gona, amma duk da haka suna da taƙaitacciyar damar samun jari da gona da sauran muhimman kayan aiki.



### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. Gwamnatin Tarayya da ta Jihohi su gano su kuma yi maganin duk wani nau'i na rashin daidaito a fannin noma da ake da shi a tsakanin mata da maza da mutane masu buƙata ta musamman.
2. A shigar da ƙa'idodjin da za su ba wa kowa dama bai ɗaya a shirin faɗaɗa aikin noma a kuma magance damuwarsu.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A samar da damar samun tallafin fasahar zamani ga mata don a inganta samar da kaya, da rayuwa da kuɗin shiga.

4. A ba da horo a fannin tattara bayanai a kan maza da mata da masu buƙata ta musamman a ɓangaren noma, waɗanda za a riƙa nazarinsu a ware, haɗi da matsayinsu.

5. A haɓaka haɗin guiwa tsakanin gida da waje.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a dukkan matakai.

Kwamitocin Majalisun Tarayya.



Makarantun Aikin Gona.

Kungiyoyin manoma na ƙasa da na jiha.



Ma'aikatun Tarayya da na jiha, da suke da alhakin tsara al'amura da aikin gona da cigaban karkara da harkokin mata da harkokin kuɗi da kasafin kuɗi.



*Samarwa daga*
*Ƙungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# (B). Ayyukan da ba na Gwamnati ba (Ba Aikin Gona Ba) da Aikin Gwamnati

## Halin da ake Ciki:

1. Ma'aikatan da ba na gwamnati ba a fannin tattalin arziki a Nijeriya sun haɗar da mata kaso **60-79 cikin ɗari** amma a ɓangaren aikin gwamnati maza sun fi yawa.



2. Dokokin aiki a Nijeriya ba sa kare mata da nuna musu wariya ba.

3. Akwai mata da yawa a ɓangaren ƙanana kasuwanci amma maza sun mamay matsakaita da manyan kasuwanci.

## Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A shigar da damuwar mata da maza da 'yammata da yara da masu buƙata ta musamman a dukkan ɓangarorin aikin yi a Nijeriya.

2. A yaba a kuma ƙarfafa guiwar Tsarin Kasuwanci Mai Kula Da Al'umma (CSR), waɗanda suka magance damuwar mata da maza da 'yammata da yara da Masu Buƙata ta Musamman da kuma tallafa wa matsakaita da ƙananan masana'antu.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

3. A gudanar da gangami a kuma ɗauki matakin sake bitar dokoki da manufofin aiki don su dace da ƙa'idojin Daidaiton Jinsi da inganta rayuwar mata da shigar da kowa cikin zamantakewa.
4. A samar da dokar jinsi ta wajen aiki don a kawar da tuhuma da tarnaƙi ga mata da sauran rukunan da ba su da dama a wajen aikin.
5. A samar da yanayin da zai kawar da rashin daidaiton jinsi da tarnaƙi.
6. A kafa ƙwararan ƙa'idojin ɗaukar mataki da za su ware kaso 60 cikin ɗari na tallafin ƙananan masana'antu ga mata.
7. A ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki a kan naɗin shugabanni don ya kula da jinsi da yanki da tsara da buƙata ta musamman da kuma addini ba tare da yin watsi da cancanta ba.
8. A samar da tallafi don shigar mata cikin Yankin Ciniki Kyauta na Nahiyar Afrika (AfCFTA)

## Masu Ruwa da Tsaki

- Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.
- Hukumomi da Ma'aikatun Gwamnati musamman Ma'aikatar Harkokin Mata.
- Kungiyoyin Kare Haƙƙoƙin Mata da sauran ƙungiyoyin fararen hula
- Ma'aikatu masu zaman kansu.
- Majalisun Tarayya.

# ( C). Wasanni da Motsa Jiki

## Halin da ake Ciki:

1. Dokoki a fannin wasanni suna nuna wariya ga shigar mata da kula da harkokin wasanni da biyan albashi.

2. Fannin nishaɗantarwa yana da damar samar da kyakkyawan sauyi don gyara tasirin munanan al'adu da halayyar al'umma da tsare-tsare da kuma aiwatarwa.

3. Maza sun mamaye fannin nishaɗantarwa a kafofin sadarwa, wanda hakan ya sa suke da ƙarin damar samun kuɗaɗe fiye da mata kuma ba lallai su iya fahimtar shaidancin ɗaukar mata a matsayin abubuwa ba.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A samar da kuɗaɗe na musamman don mata da masu buƙata ta musamman su gina iyawarsu.

2. A ƙirƙiro ayyukan wasannin da matasa za su shiga a wuraren da ake da matsi a kuma yi amfani da kuzarinsu don kasuwanci mai amfani.

3. A haɗa gangami don kawar da rashin daidaito a wajen biyan kuɗi da damammaki dangane da jinsi ko buƙata ta musamman a fannin wasanni.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

4. A samar da doka da za ta ba wa kowa, mata da maza da 'yammata da yara da masu buƙata ta musamman, dama bai ɗaya a ɓangaren wasanni da nishaɗantarwa.
5. A tabbatar da yadda ake amfani da harshe a wasanni da kafafen sadarwa bai nuna wariya ga kowane jinsi ba.
6. A horar da masu kula da wasanni da jami'ai da 'yan jaridu a kan batun jinsi.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta jahohi.



Kungiyoyin Fararen hula.



Hukumar Kididdiga t Kasa.



Kafafen sadarwa.



Ma'aikatu da Hukumomin da suke kula da wasanni da nishaɗantarwa.



Ma'aikatu masu zaman kansu.

# (D) Ayyukan Kula da ba a Biya da Tattalin Arziƙin Magidanta

## Halin da ake Ciki:

1. Ba a ɗaukar ayyukan mata na gida a matsayin wani aiki mai muhimmanci da yake haɗe da dokar jama'a da kasuwanci masu amfani.
2. Nauyin da ke kan mata a matsayin iyaye yana taimaka wa bunƙasar ma'aikatan ƙasa amma ba a la'akari da shi a wajen tsare-tsaren ƙasa.
3. Ba a biya kuma ba a yaba wa da ayyukan da mata suke yi na kulawa.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. Kungiyoyin Kare Haƙƙoƙin Mata su yi aiki da kafafen sadarwa don kai rahoto dangane da ƙa'idoji da batutuwan GEESI.
2. Iyalai su koya wa yara da 'yammata girmama jinsi.
3. A yi fafutuka da wayar da kai a ƙasa don kawar da gudanar da al'adun nuna wariya ga mata da 'yammata.
4. A tabbatar da an yi fafutuka da samar da ƙuduri a wajen tallafa wa da ba wa mazaje hutun haihuwa a aikin gwamnati, da ɓangaren masu zaman kansu da ƙungiyoyin al'umma.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*
MacArthur Foundation

5. Gwamnati da ƙungiyoyin al'umma su ƙara wayar da kai don tabbatar da damar samun hanyoyin tsarin iyali marasa haɗari da kuma zaɓi.

6. Masu kafafen sadarwa da gwamnati da ɓangaren masu zaman kansu da ƙungiyoyin al'umma da abokan kawo cigaba su ɗore a kan fafutukar sauyi a game da jinsi don cigaban ƙasa.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.



Kungiyoyin fafutukar kare haƙƙoƙin mata da na al'umma.



Iyalai

Ɓangaren masu zaman kansu.



- Kafafen yaɗa labarai.
- Abokan kawo cigaba.

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA UKU:
# BUNƘASA ƊAN'ADAM

## (A). Kiwon Lafiya da Rayuwa da Cimaka

### Halin da ake Ciki:

Yaran Nijeriya suna fama da matsalolin cin zarafi daban-daban, duk da cewa akwai Dokar Haƙƙokin Yara ta shekarar 2003 da kuma Kudurin Gwamnatin Tarayyar Nijeriya na Hadaɗɗen Tsarin Gina Yara na shekarar 2007.

### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A samar da tsarin shigar da maganar jinsi a ɓangaren kiwon lafiya.
2. A mayar da hankali wajen yin manufofi da tsara shirye-shirye a kan kula da lafiya a ɓangaren renon ciki da goyo ga buƙatar kowa tare da ɗaukar matakai da samar da kuɗaɗen da za su auna ƙwazo.
3. A gudanar da gangami a kan tsarin iyali da tazarar haihuwa a harsunan gida.
4. A samar da Cibiyoyin Kula da Waɗanda Aka Ci Zarafi (SARCs) na ƙasa da wurin zama (wuri mai aminci) ga waɗanda suka tsira daga nuna musu rashin imani dangane da jinsi da jima'i (SGBV).



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

5. A samar da SARCs a wurare masu nisa, a kuma wayar da kan masu fafutuka a cikin ƙananan al'ummomi game da SGBV.
6. A samar wa da SARCs dukan kayan aikin da suke buƙata, a matsayin wata mai iya kai ɗauki a matakin farko a yanayin rikici.
7. A sanya hannun jari a kan irin cimaka, wanda za a iya gabatar da shi a cikin shirin ciyar da yara a makarantu da kuma jerin alfanun noman gargajiya.
8. A faɗaɗa shirin ciyarwa a gida zuwa makaranta zuwa ga dukkan faɗin ƙasa.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jihohi.

Kungiyoyin Fararen Hula.

Abokan Kawo Cigaba na Kasa da Kasa.



Hukumar Kula da Lafiya a Matakin Farko.



Ma'aikatun Lafiya da na Ilimi da na Aikin Gona da na Harkokin Mata da na Harkokin Jin Kai da na Kula da Annoba da na Cigaban Al'umma, na Tarayya da na Jihohi.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

# (B). Lafiyar Renon Ciki da Goyo da HIV da COVID-19

## Halin da ake Ciki:

1. Mata da 'yammata da mutane masu buƙata ta musamman da 'yan gudun hijira da waɗanda rikici ya raba su da gidajensu da yara da masu tasowa da tsofaffi da tsirarun ƙabilu ko mabiya addini ko jinsi da mutanen da ba su da wata shaida a hukumance da masu ɗauke da cutar HIV (PLWHA) duk suna cikin haɗarin fuskantar tsangwama da nuna musu wariya.

2. Mata da 'yammata sun fi shiga haɗarin kamuwa da HIV.

3. Ana samun ƙaruwar rashin lafiyar tunani da yawan kashe kai a tsakanin matasa da masu wadata, wanda ake alaƙanta hakan da yanayin tattalin arziƙin zamantakewar ƙasa.

4. Nijeriya ita ke da kaso 2.64 na mutanen duniya amma tana da adadin kaso 20 cikin ɗari na yawan mace-macen mata a duniya a yayin renon ciki da goyo.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A sake duba dokokin da suka danganci lafiyar renon ciki da goyo da kuma Nuna Rashin Imani Dangane da Jinsi don a magance wuraren da ake da rauni.
2. A tabbatar da ɗorewar amfani da tsarin jinsi a ɓangaren samar da kiwon lafiya da tsarin kula da lafiya.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Hakkin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A daidaita kasafin kuɗi da ma'aunan ƙwazo.
4. A gudanar tsari mai dogon zango ga tsarin kula da lafiya, wanda zai magance buƙatun mata da maza don a tabbatar da samar da ayyuka ba tare da haɗari ba.
5. A sauya tsarin kai ɗaukin gaggawa a fannin kula da lafiya na ƙasa.
6. Gwamnati da Kungiyoyin Fararen Hula su ƙara wayar da kan mutane a kan hanyoyin tsarin iyali marasa haɗari da yin zaɓi, a kuma tabbatar da samar da dama ga kowa.
7. A samar da bayanai a kan jinsi, wanda za a yi nazarin su a ware, da kuma kayan aikin da za a kai ayyuka ga talaka cikin sauri.
8. A horar da jami'an lafiya da suke da masaniya game da bambance-bambancen jinsi da daidaito don su kula da batun jinsi a wajen samar da kiwon lafiya.
9. A shigar da ilimin jima'i a shirye-shiryen matasa da manhajar makarantu don rage samun juna biyu a tsakanin matasa.

## Masu Ruwa da Tsaki

- Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.
- Ma'aikatun Ilimi da na Lafiya da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jahohi.
- Kungiyoyin Al'umma.
- Majalisun Tarayya.
- Majalisar Likitoci da Likitocin Haƙora ta Nijeriya.
- Hukumar Kula da Jami'o'i ta ƙasa
- Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

## ©. Kula da Lafiyar Uwa da ta Yaro ko Cigaban Yaro

### Halin da ake Ciki:

1. Mata suna matuƙar rasa damammaki a ɓangarorin rayuwa da dama a Nijeriya.

2. Duk da shirye-shiryen tallafin lafiya da yawa, har yanzu adadin mace-macen mata masu juna biyu a Nijeriya yana da yawa kuma ya yi nisa da abin da ake son cimma a Muradun Cigaba Mai Ɗorewa na 3, wato ƙasa da mutuwa 70 a duk haihuwa 100,000 nan da shekara ta 2030.
3. Mata daga yankunan karkara da kuma Arewacin Nijeriya sun fi shiga haɗarin mutuwa a wajen haihuwa idan aka kwatanta da takwarorinsu da ke birane da kuma Kudanci saboda yawan haihuwa da kuma wasu batutuwa na al'ada.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. Gwamnati da ƙungiyoyin al'umma su ƙara wayar da kai su kuma tabbatar da damar samun hanyoyin tsarin iyali da zaɓuɓɓuka marasa haɗari.
2. A ƙara yawan gangami a kan kula da ƙananan yara, haɗi da yin rigakafi.

3. A sake duba dokokin kiwon lafiya don su kai matsayin na ƙasa da ƙasa a wajen kula da masu juna biyu da ƙananan yara.

4. Kungiyoyin fararen hula da gwamnati su tsara yadda za a tunkari harkar kula da lafiya, wanda mutane suka fi karɓa kuma a shigar da masu amfana a cikin tsarin.

5. A yi amfani da darussan da aka koya daga tsarin Tura Kuɗl don Kula da Lafiyar Masu Juna Biyu da Kananan Yara na SURE-P don a ƙara wasu shirye-shiryen tura kuɗi bisa sharaɗi, wadan za a yi don mata da masu buƙata ta musamman da wasu rukuni na musamman.

6. A yi fafutukar shigar da karatun jinsi a manhajojin makarantu a kowane mataki.

7. A ƙara yawan bincike a kan jinsi da kuma yin amfani da ƙididdigar jinsi wajen yin dokoki da tsare-tsare a kowanne ɓangare.

8. A aiwatar da shirin zaburar da alumma don sauya tunani game da halayyar mata da maza da 'yammata da yara don inganta lafiyar uwa da ta yara.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jihohi.



Kungiyoyin Fararen Hula.



Ma'aikatun Ilimi da na Lafiya da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jihohi.

Hukumar Kula da Lafiya a Matakin Farko da Hukumomin Samar da Cigaba.



# (D). Tsarin Jinsi da Kiwon Lafiya

## Halin da ake Ciki:

- Tsarin samar da ayyukan kula da lafiya da ake da shi yanzu ba shi da dabaru da kayan aikin da zai magance rashin daidaiton jinsin da ake da shi wajen damar samun kula da lafiya da kuma ingancin ayyukan da ake da su.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:


1. A aiwatar da tsarin kula da lafiya da zai rage tasirin matsalolin lafiya a kan iyalai, musamman mata, a matsayin masu ba da kulawa.
2. Gwamnati ta inganta tsarin kula da lafiya a matakin farko na ƙanan hukumomi da unguwannin da kuma samar da ingantacciyar hanyar tura marasa lafiya zuwa wasu matakan na kula da lafiya.
3. A aiwatar da tsararrun bayanai a kan maza da mata, waɗanda za a riƙa nazarinsu a ware a dukkan ma'aunan ɓangarorin kula da lafiya.
4. Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa su ci gaba da taka muhimmiyar rawa wajen jagorantar ƙasar da tsarawa da aiwatar da tsarin samar da kula da lafiya da zai magance buƙatun kowa.
5. Gwamnati ta yi haɗin guiwa da ƙungiyoyin addini don ƙara wayar da kai game da batutuwan jinsi a fannin kula da lafiya da rage ko kawar da tsangwama da take tattare da cutar HIV da sauran batutuwan da suka shafi renon ciki da goyo da yawanci suke shafar mata.

6. A ƙara saka hannun jari a ɓangaren kula da lafiya, wanda zai inganta walwalar mata da ƙwararru a fannin kula da lafiya don cimma matakin ƙasa da ƙasa da aka amince da shi.

7. A samar da dokoki da tsare-tsare don a tabbatar da al'adar adalci da daidaito a dukkan hukumomin gwamnati da tsarin gwamnati da masu zaman kansu da al'ummomi, wajen mu'amala da kiwon lafiya da cimaka da matsalolin sadarwa.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.



Ɓangaren Masu zaman Kansu.



Ma'aikatun Ilimi da na Lafiya da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jihohi.

Hukumar Kula da Lafiya a Matakin Farko.





Al'ummomi.



Abokan Kawo Cigaba na Kasa da Kasa.



Kungiyoyin Addinai.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

## (E). Samun Ilimi da Dabarun Sana'a da na Rayuwa

### Halin da ake Ciki:

1. Akwai ƙaruwar daina zuwa makaranta, musamman a tsakanin 'yanƙasa mata, saboda samun juna biyu da yarinta.
2. Ana taƙaita shigar da bayanan Daidaiton Jinsi da Inganta Rayuwar Mata da Shigar da Kowa a Zamantakewa, a fannin Koyo da Koyarwa.
3. 'Yammata suna yin aikace-aikacen gida da yawa don haka ba su da lokacin yin aikin gida da aka ba su a makaranta.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A ƙarafafa ƙara sa yara mata a makarantu, a mayar da yin talla ya zama laifi, a kuma samar da tallafin kuɗi ga iyaye talakawa.
2. A yi amfani da tsarin jinsi wajen sa ido da auna ƙwazon makarantu ko na ilimi da sa yara a makaranta da kuma ƙiriniya.
3. A yi fafutuka a kan, kuma a samar da tallafin ƙwararru don bunƙasa karatun jinsi da shigar da kowa, a manhajar makarantu ta ƙasa a kowane matakin ilimi.
4. A samar da tallafin kuɗi ga mata ko 'yammata don su riƙa shiga kwasakwasan da suka mayar da hankali ga kimiyya ko fasaha.
5. A yi amfani da fasaha a inganta damar da mata ko 'yammata suke da ita na samun ilimi da koyo.
6. A ƙara sanya hannun jari a ɓangaren ilimin sana'a da fasaha.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*
MacArthur Foundation

7. A ƙara sanya hannun jari a ɓangaren ilimi don inganta shigar 'yammata da masu buƙata ta musamman da yaran da suka fito daga gidaje matalauta.

8. A tabbatar da daidaiton jinsi a Kwamitin Kula da Makarantu don kula da batutuwan jinsi yadda ya kamata a makarantu.

9. A adana bayanan ayyuka na ƙwarai don kwaikwaya da ɗabbaƙawa, a wuraren suka dace.

10. A tabbatar da daidaiton jinsi a matakan ilimi daban-daban a Nijeriya.

11. A ba da fifiko ga ilimantar da 'yan ƙasa daga tushe, haɗi da ilimin manya ga maza da mata.

12. A tabbatar da samun dama bai ɗaya, don yin karatun manyan digiri, ga mata da maza da kuma kulawar da ta wajaba a wajen aiki.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.



Kungiyoyin Fararen Hula.



Ma'aikatun Ilimi da na Lafiya da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jahohi.

Iyaye da iyalai.





Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

## (F). Tsarin Ba da Kariya a Zamantakewa

### Halin da ake Ciki:

1. Rikece-rikicen jin ƙai da ake da su a Nijeriya, waɗanda suka samu a dalilan rikici tsakanin al'ummomi da tashin hankali da sauyin yanayi da ambaliyar ruwa a kai-a kai da dabarun kan mai uwa da wabi da jami'an tsaro suke amfani da su wajen yaƙar ayyukan ta'addanci da sauran su.
2. Rikicin makamai a ƙasar ya yaɗu zuwa ga rikicin tsakanin manoma da makiyaya da 'yan fashi da makami da masu satar mutane, waɗanda hakan suka jefa fararen hula cikin yanayi na tashin hankali.
3. Mata da yara sun fi shan wahala a wannan mummunan yanayi, tun da nuna rashin imanin jima'i da na jinsi da auren wuri su yake shafa.
4. Nijeriya tana mataki na 11 a masu yawan auren wuri a duniya, kuma tana mataki na uku a duniya a masu yawan matan da suka yi aure ko suka fara zaman tare kafin su kai shekara 18.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A tabbatar da bincike mai ɗorewa don a fahimci dalilan da suke haifar da tashin hankali da yanayin shiga haɗari da kuma tasirin yaɗuwar ƙananan makamai, cikin gaggawa, a kan tsaron mata a zahiri da zamantakewa.
2. A gudanar da gwaji na gaskiya a kuma biya al'ummomin da aka haƙi ma'adanai a wurarensu, idan an sami gurɓatar muhalli ko take haƙƙoƙi.
3. A tabbatar da ƙarin cikakken kai ɗauki, haɗi da ilimantarwa game da haɗarin hijira ba bisa ƙa'ida ba da samar da tartibin tallafi ga waɗanda suke nufin yin hijira da kuma ƙarfafa hukumomin gwamnati don cikakken haɗin guiwa.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

4. A inganta adadin yawan 'yansanda daidai da mutane don gudanar da aikin ɗansanda yadda ya kamata da kuma bayar da horo da kuɗaɗe ga jami'an 'yansanda da suke aiki a ƙarƙashin yanayin jin ƙai da rikici ya haifar.
5. A kafa wani asusun na waɗanda suka tsira daga tashin hankalin jinsi, a kuma shigar da waɗanda abin ya shafa ko waɗanda suka tsira a wajen tallafin magance firgici don su dawo cikin hayyacinsu.
6. A ƙarfafa aikin Cibiyoyin Tura Waɗanda aka Ci Zarafinsu ta Jima'i (SARCs) a dukkan jahohi don a samar da ayyukan da suka dace da na gaggawa.
7. A mayar da hankali ga kula da lafiyar tunani da ta ƙwaƙwalwa da zamantakewa da ruhi, waɗanda za su karkata ga kawar da tsangwama da ta danganci lafiyar ƙwaƙwalwa, a kuma wayar da kai game da matakan da suka dace kowa ya ɗauka don samo maganin cutarsu.
8. A ɗorar da fifita tallafin kariya a zamantakewa don a rage talauci da rashin dama a tattalin arziƙin zamantakewa, a kuma ƙarfafa biyan kuɗi daga gwamnati zuwa mutum ta na'ura da shigar da kowa a harkar kuɗi.
9. A tsara a kuma aiwatar da dabarun aiki da sarakunan gargajiya da shugabannin addinai daga rukunin kowane jinsi don a horar a kuma shigar da GEESI a tsarin shari'ar gargajiya.
10. A samar da gudummawar kuɗi ko wata gudummawar daban don samarwa da kula da gine-gine.
11. A yi amfani da fasaha wajen haɓakawa da inganta ayyukan gwamnati don amfanin 'yan ƙasa.

## Masu Ruwa da Tsaki

- Sarakuna da shugabannin addinai.
- Gwamnati a kowane mataki.
- Hukumar Kula da Katin Ɗan Kasa.
- Hukumar Kula da Aikin 'Yansanda.
- Kungiyoyin Fararen Hula.
- Ma'aikatar Sadarwa da Tattalin Arzikin Na'ura.
- Abokan Kawo Cigaba.
- Majalisun Tarayya.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

# (G). Jinsi da Buƙata ta Musamman

## Halin da ake Ciki:

1. Mutane masu buƙata ta musamman (PWDs) suna fama da tauye haƙƙoƙin ɗan'adam daban-daban, hadi da tsangwama da nuna musu wariya da tashin hankali da rashin samun damar kula da lafiya da muhalli da ilimi.

2. Yanayin yana ƙazanta idan mata da 'yammata suna da buƙata ta musamman. Suna fuskantar tarnaƙi guda uku wajen samun cikakken daidaito da cigaba, waɗanda suka haɗar da zama mata da talauci da kuma buƙata ta musamman.

3. Kasa da kaso 5 cikin ɗari na yara da matasa masu buƙata ta musamman ne suke da damar samun ilimi da horo.

4. Mata masu buƙata ta musamman sun fi fama da rashin kyakkyawar mu'amala da cin zarafi fiye da matan da ba su da buƙata ta musamman.

5. Dokar Hana Nuna Wariya Ga Masu Buƙata ta Musamman ta shekarar 2018 ta kasa magance buƙatun mata na musamman da 'yammata, waɗanda suke fuskantar matsi iri daban-daban saboda jinsinsu da kuma buƙata ta musamman da suke da ita.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A yi haɗin guiwa a tallafa wa Hukumar Kula da Masu Buƙata ta Musamman don ta tsara dokoki da shirye-shirye dangane da daidaiton jinsi da inganta rayuwar mata da aƙidun tafiya da kowa da kuma auna tasirin su.

2. A aiwatar da dokar gine-gine, wadda ta nemi cewa dole dukkan gine-ginen gwamnati su ba da damar shiga ga mutane masu buƙata ta musamman.

3. A gudanar da gangami don wuraren aiki su tabbatar da cewa mutane masu buƙata ta musamman sun sami haƙƙi da damammaki daidai da kowa.

4. A yaɗa rohoton shekara a kan masu buƙata ta musamman daga Hukumar Kula da Masu Buƙata ta Musamman ga mutanen da suke da buƙata ta musamman da ma sauran al'umma bakiɗaya.

5. A ƙara samar da kuɗin gwamnati na makarantun masu buƙata ta musamman.

6. Kungiyoyin da ba na gwamnati ba su gudanar da gangami don magance tsangwamar masu buƙata ta musamman a kuma ƙara wayar da kai game da nau'o'in buƙata ta musamman, musamman waɗanda suka shafi basira.

7. Hukumar Kula da Masu Buƙata ta Musamman ta adana ta kuma yaɗa rumbun adana bayanai a yanar gizo na ƙungiyoyin da suke tallafa wa yara masu buƙata ta musamman.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.

Ma'aikatun Aiki da Gidaje da na Ilimi da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jahohi.

Hukumar Kula da Masu Buƙata ta Musamman.

Kungiyoyin da ba na gwamnatiba da na fararen hula.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA HUƊU: GEESI A WASU MUHIMMAN CIBIYOYIN ƁANGARORIN ZAMANTAKEWA

## (A). Ruwa da Tsafta

### Halin da ake Ciki:

1. Ayyukan samar da ruwa da tsaftar jiki da ta muhalli ba su da kyau a Nijeriya.
2. Karancin samar da ruwa yana ƙara haddasa matsaloli ga mata da yara, musammam a yankunan karkara.
3. Har yanzu Nijeriya tana cikin jerin ƙasashen da ake bayangida a bainar jama'a, wanda hakan yake shafar lafiyar mata da ta 'ya'yansu.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A horar da ma'aikatan fannin samar da ruwa a kan kula da damuwar kowa da abin da kowa yake sha'awa.
2. A tabbatar da ƙa'idojin yin kasafin kuɗi da za su tabbatar da ana raba albarkatun ƙasa ga kowa cikin adalci a tsare-tsaren ɓangaren samar da ruwa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A samar da magwajin jinsi da bayanai game da maza da mata, waɗanda za a riƙa nazarinsu a ware don a tabbatar da amfani da albarkatun ruwa cikin adalci.

4. A ƙarfafa shigar mata a wajen tsara doka da aiwatarwa a ɓangaren Samar da Ruwa da Tsaftar Muhalli da ta Jiki.

5. A samar da dabarun shigar da tsarin samar da ruwa don kula da buƙatun kowa.

6. A yi aiki tare da Majalisun Tarayya don a yi amfani da wani tsari da yake la'akari kuma ya haɗar da buƙatun mata da maza da 'yammata da yara a wajen samar da kuɗin haƙa rijiyoyin burtsatse da sauran ayyukan da suka danganci samar da ruwa a yankunansu.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jihohi.

Ma'aikatun Albarkatun Ruwa da na Harkokin Mata na Tarayya da na Jihohi.



Majalisun Tarayya.



Kungiyoyin Fararen Hula.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# (B). Samar da Gidaje

## Halin da ake Ciki:

1. Maza sun fi mallakar gidaje a kan mata kuma mata da yawa suna zaune a gidajen da ba su dace ba.
2. Nijeriya tana da ƙarancin gidaje na mutum miliyan 20 tun a shekarar 2020.
3. A cikin duk mata 10 kimanin mata 7 ba su da damar samun kyakkyawan banɗaki kuma mata da 'yammata da sauran rukunin marasa galihu suna fuskantar haɗari ga lafiyarsu da kuma cin zarafi.
4. Dokar Samar da Gidaje ta Kasa ba ta magance matsalar rashin daidaito a damar samun fili da kuɗi da sauran hanyoyin inganta rayuwa ba.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A shigar da maganar jinsi a cikin Dokar Samar da Gidaje.
2. A yi amfani da kasafin kuɗin da zai tabbatar da rabon albarkatu cikin adalci ga mata da maza da 'yammata da yara da sauran rukunin marasa galihu a kowanne matakin gwamnati da cibiyoyi da samar da kuɗi don aiwatar da Tsarin Samar da Gidaje na Kasa.
3. A cire dukkan tarnaƙi da mata da sauran rukunin marasa galihu suke fuskanta a wajen samun bashin gina gida.

4. A tallafa wa samar da kuɗi da kafa Hukumar Samar da Gidaje ga Mata.
5. A shigar da mata a wajen sa ido da bibiyar kuɗaɗen da aka ware bisa Dokar Samar da Gidaje ta Kasa don tabbatar da yin komai a buɗe, da ɗaukar nauyi da ƙimanta kuɗi.
6. A yi aiki tare da gwamnatin jiha don a saukaƙa samun takardun fili ga mata ba tare da yin la'akari da matsayin aure ba.
7. A yaɗa manufa zuwa gwamnatin jiha da ta ƙaramar hukuma da sarakunan gargajiya a kan mata su mallaki ƙasa ko yi gado.
8. A shigar da sarakuna ko shugabannin al'umma a wajen aiwatar da Tsarin Samar da Gidaje na Kasa.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta jihohi.

Gwamnatin Jahohi da ta kananan hukumomi

Shugabannin Gargajiya.



Kungiyoyin kare haƙƙoƙin mata da sauran ƙungiyoyin fararen hula.

Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje ta Tarayya.

Bankin Samar da Gidaje na Tarayya.

Babban Bankin Nijeriya.

## (C). Jinsi da Muhalli da Sauyin Yanayi

### Halin da ake Ciki:

1. Mata sun fi shiga haɗarin annobar da ta shafi yanayi fiye da maza.
2. Yanayin Muhalli yana shafar mata da maza da mutane masu buƙata ta musamman ta hanyoyi mabambanta duba da rawar da suke takawa da kuma gwargwadon ƙarfin yanke hukunci.
3. Mata da hanyoyin samun kuɗin shigarsu suna fuskantar haɗarin da lalata muhalli ya haifar da shi.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A yaɗa a kuma tallafa wa shirye-shiryen da za su rage tasirin sauyin yanayi a kan mata da sauran rukunin marasa galihu.
2. A horar da mata da sauran rukunin marasa galihu a kan amfani da muhalli yadda ya kamata.
3. A ƙara yawan damar da mata suke da ita ta samun bayanai da dabarun sadarwa a kan jure wa sauyin yanayi, wato iya hangen abin da ka zo da kai ɗauki da iya murmurewa daga tasirin sauyin yanayi.
4. A auna tasirin lalacewar muhalli a kan mata da sauran rukunin marasa galihu, a kuma tsara ko aiwatar da matakai don dawowa ko murmurewa daga sauyin yanayi.

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.



Hukumar Agajin Gaggawa ta Jiha (SEMA) da sauran hukumomi.

Kungoyoyin kare haƙƙoƙin mata da sauran ƙungiyoyin fararen hula.



## (D). Kafafen Sadarwa

### Halin da ake Ciki:

1. Maza sun mamaye harkokin kula da kafafen sadarwa ta yadda ba a ba mata dama, kuma shirye-shiryensu suna nuna mata a matsayin wani kaya.

2. Ba wata jarida mai fita kullum da take mallakin mace a Nijeriya ko da yake akwai gidajen rediyon mata kaɗan.

3. Kafafen sadarwa sun gaza wajen haɓaka shirya rahotonnin da suke kula da jinsi.

4. Yadda maza suke juya al'umma, da ƙarancin kuɗi sun ware mata daga ɓangaren kafafen sadarwa, ba kuma ƙwarewa suka rasa ba.

5. Wasu lokutan masana'antun nishaɗantarwa suna nuna mata da matantaka da buƙata ta musamman ta hanya mara kyau.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A shigar da batun jinsi a dokokin kafafen yaɗa labarai da shirye-shirye.

2. A tabbatar cewa mata da maza haɗi da masu buƙata ta musamman suna da dama bai ɗaya ga samun bayanai da 'yancin faɗin albarkacin baki da kai rahoto.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A yi amfani da nazari bisa ƙa'idodjin daidaiton jinsi da ingata rayuwar mata da shigar da kowa a zamantakewa (GEESI) a rahoton kafafen sadarwa don a tabbatar da jin bakin kowa a rahoto.

4. A samar da tallafin kuɗi da kayan aiki ga mata don mallakar kafafen sadarwa.

5. A gudanar da horo a kai-a kai don ƙarfafa horo ga kafafen sadarwa da aikin jarida na bincike don a yi la'akari da sha'awa da kuma damuwar kowa, hadi da mata da rukunin marasa galihu.

6. A naɗa jami'in kula da jinsi ko shigar da kowa, a ɗakunan yaɗa labarai na kowace kafar sadarwa.

7. A sanya takunkumin da ya dace a kan yaɗa rahoton aibanta mata da zawarawa da mutane masu buƙata ta musamman da sauran rukunin marasa galihu, ta kafafen sadarwa da na sada zumunta.

## Masu Ruwa da Tsaki

Kungiyar Gidajen Rediyo da Talabijin ta Nigeriya.

Kungiyar Editoci ta Nijeriya.

Ma'aikatun Sadarwa da na Harkokin Mata.

Hukumar Kula da Gidajen Rediyo da Talabijin.

- Kungiyar 'Yan Jaridu ta Nijeriya.
- Kungiyar 'Yan Jaridu Mata ta Nijeriya.

Majalisar Kula da Tallace-tallace a Kafafen Sadarwa (ARCON).

Masu Zaman Kansu

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA BIYAR:
# GEESI A ƁANGAREN TSARO

## GEESI A Ma'aikatun Tsaro

### Halin da ake Ciki:

1. Akwai ƙarancin wakilcin mata a ɓangaren tsaro.
2. Shigar da ra'ayin jinsi a ɓangaren tsaro yana da muhimmanaci wajen cimma gudanar da aiki yadda ya kamata da kuma mutuncin ɓangaren.

### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A samar da ƙwarewa don shigar da batun jinsi a ɓangaren tsaro.
2. A samar da rumbun adana bayanai dangane da ƙa'idojin GEESI don yin doka da tsarawa da magwajin ƙwazo.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A duba dokokin da ake da su, waɗanda suka dace da duniya da yankuna da ƙasa don kawar da dukkan saɗarorin nuna wariya don su dace da ƙa'idojin GEESI.

4. A inganta fahimtar jami'an kula da jinsi a dukkan ma'aikatun tsaro a kan batutuwan jinsi da kuma ƙwarewar da ake buƙata.

5. A shigar da batun jinsi a dabarun daidaita jinsi a dukkan kayan karatu da manhaja a ma'aikatun tsaro.

6. A horar da jami'an jinsi a kan amfani da ma'aunan kula da jinsi da yin nazarin bayanai a kan maza da mata a ware.

7. A ba wa ma'aikatan ɓangaren tsaro horo a wajen amfani da kasafin kuɗi, wanda yake kula da buƙatun kowa, haɗi da mata da 'yammata da maza da yara da masu buƙata ta musamman.

8. A adana a kuma yaɗa labaran matan da suka nuna ƙwazo da gudummawar 'yammata a wajen warware rikici da samar da zaman lafiya.

9. A samar da ƙarin yanayi mai daɗi ga matan da suke aiki a ɓangaren tsaro.

10. A samar da kayan aiki don tallafa wa ƙarin mata don shiga tsarin gargaɗi a kan kari da kai ɗauki a kan kari a cikin al'ummomi.

11. A horar da matan da suke shiga maganar warware rikici.

12. A ƙarfafa guiwar haɗin kai tsakanin gwamnati da ƙungiyoyin fararen hula don ba da horo a kan samar da zaman lafiya da yin gargaɗi a kan kari da kai ɗauki a kan kari ga mata da rukunin matasa a cikin al'ummomi.

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnatin Tarayya da ta Jahohi.



Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.



Sojoji da 'yansanda da sauran hukumomin tsaro.

Ma'aikatun Harkokin Mata na Tarayya da na Jahohi.



Kungiyoyin Fararen Hula.

# (A). Maganin Ta'addanci da Rikici da Dawwamar da Zaman Lafiya

## Halin da ake Ciki:

1. Nijeriya tana fuskantar matsalolin tsaro iri-iri, tare da mummuna tasirin hakan ga mata da yara.
2. Mata da yammata sun fuskanci duk wani nau'in cin zarafi, haɗi da kame su da nuna rashin imani ta jima'i da asarar rayuka da ta hanyoyin samun kuɗin shiga da hana 'yammata karatu da raba su da gidajensu.
3. Akwai rashin ingantaccen aiwatar da ajandar mata da zaman lafiya da tsaro saboda ɗabi'un zamantakewa na babakeren maza da juya al'amaura da rashin ƙwaƙƙwarar madogara a shari'ance da ƙaruwar yi wa mata ƙarfa-ƙarfa da danne su a hanyoyin samar da zaman lafiya da warware rikici.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A gudanar da ayyukan yaɗa manufa a kan SGBV ga 'yammata da mata a yankunan da ake rikici, inda za a nufi masu yin doka da jami'an tsaro.
2. A ba wa jami'an tsaro da mata da matasa horo a kan tsarin cimma UNSR 1325 da UNSR 2250 a kan zaman lafiya da tsaro.
3. A shigar da batun jinsi a tsarin yin aiki da mutanen da aka raba su da gidajensu.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙkin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

4. A ba wa mata horo don a ƙarfafa matsayinsu da kuma gudummawarsu wajen warware rikici.

5. A ƙarfafa haɗin guiwa tsakanin gwamnati da Kungiyoyin Fararen Hula wajen ba wa mata da matasa horo a kan gina zaman lafiya da kuma gargaɗi a kan kari da kai ɗauki a kan kari a cikin al'umma.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.



Sojoji da 'yansanda da sauran hukumomin tsaro.

Ma'aikatun Harkokin Mata na Tarayya da na Jahohi.

Hukumar Kula da 'Yan Gudun Hijira da waɗanda aka raba su da gidajensu.



UNHCR da sauran abokan kawo cigaba.

Hukumar Agajin Gaggawa ta Kasa

Kungiyoyin yaɗa manufa da sauran Kungiyoyin Fararen Hula.



- Hukumar Agajin Gaggawa ta Jiha

# (B). Kula da Ayyukan Jin Kai na Gaggawa Masu Sarkakiya

## Halin da ake Ciki:

1. Akwai 'yan gudun hijira sama da **miliyan 2.9** a Arewa Maso Gabashin Nijeriya.

2. Mata da 'yammata da mutane masu buƙata ta musamman suna shan wahala fiye da yara maza a lokacin annoba amma zai yi wahala a sa su a mambobin kwamitoci ko wasu hukumomi da ake kafa wa don su magance annoba.

3. Da wuya a yi la'akari da ra'ayin mata da sauran rukunin marasa galihu sannan kuma da wahala a magance buƙatunsu da abin da suke sha'awa.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A wayar da kan masu yanke hukunci da masu ba da kulawa da ma'aikatan gwamnati wajen yin aiki da hanyoyin da za su kula da ra'ayin kowa, haɗi da ba wa marasa galihu dama iri ɗaya ta yin amfani da wuraren al'umma, a yayin ayyukan jin ƙai na gaggawa masu sarƙakiya.

2. A ƙara wayar da kai da fahimtar da mutane da yarda da daidaiton jinsi da kuma batun kariya ga masu aiki a ɓangaren jin ƙai.

3. A sauƙaƙa shigar mata da masu buƙata ta musamman cikin ayyukan jin ƙai don samar da shirye-shiryen da za su dace da kowa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

4. A ƙarfafa haɗin guiwa tsakanin Kungiyoyin ƙasa da ƙasa da ba na gwamnati ba da hukumomin da suka mayar da hankali ga batun mata da buƙata ta musamman da ƙara kai tallafi yadda ya kamata, wanda kuma zai haɗar da kowa.

5. A tabbatar da yin amfani da alƙaluman jinsi daidai kuma yadda ya kamata da kuma bayanai game da maza da mata da masu buƙata ta musamman, waɗanda za a riƙa nazarinsu a ware don samar da shirye-shirye da ayyuka don a haɓaka adalci da ba da dama bai ɗaya ga kowa.
6. A haɓaka shigar wakilan marasa galihu a aikace, wajen gudanar da ayyuka a yayin agajin gaggawa.

7. A horara da ma'aikatan hukumomin ayyukan jin ƙai don gudanar da gwajin da ake buƙata a kai-a kai da bincike waɗanda suka mayar da hankali ga damuwar kowa a yayin ayyukan jin ƙai na gaggawa.

8. A samar da isassun kuɗaɗe don a taimaka wa masu ayyukan jin ƙai da al'ummomin da ayyukan jin ƙai na gaggawa ya shafa.

9. A samar da darussan karatu a makarantun gaba da sakandire na Nijeriya, a ɓangaren Jinsi da Ayyukan Jin Kai da Nazarin Cigaba.

## Masu Ruwa da Tsaki

1. Gwamnati a kowane mataki.
2. Kungiyoyin yaɗa manufa
3. Majalisun Tarayya.
4. Hukumar Kula da Jami'o'i ta Kasa.
5. Ma'aikatar Kula da Ayyukan Jin Kai da Annoba da Cigaban Zamantakewa.
6. Hukumar Kula da 'Yan Gudun Hijira.
7. UNHCR da sauran Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.
8. Hukumar Kai Agajin Gaggawa ta Kasa.
9. Kungiyoyin ƙasa da ƙasa, waɗanda ba na gwamnati ba.
10. Hukumar Kai Agajin Gaggawa ta Jiha.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA SHIDA:
# GEESI A DAMAR SAMUN ADALCI DA HAƘƘOƘIN ƊAN'ADAM DA SHUGABANCI

## (A). Tsarin Shari'a Mai Kula da Jinsi a Nijeriya

### Halin da ake Ciki:

1. Rashin daidaiton jinsi yana ci gaba da kasancewa a dokokin Nijeriya da tsarin shari'a.
2. Amfani da iko ba daidai ba, haɗi da kama mutane barkatai da tsare mutane ba bisa doka ba da rashin adalcin hana beli da jinkirin yanke wa wanda ake zargi hukunci da hukuncin wuce gona da iri da yin azaba da cunkoso a gidajen gyaran hali da hukunta masu laifi ba tare da yi musu shari'a ba da nuna wariya, sun ƙara munana rashin adalcin jinsi a tsarin shari'ar Nijeriya.
3. Yana da wahala a kauce wa dokokin ƙasa da suke nuna wariyar jinsi a ƙasa saboda yawan ƙabilun ƙasar da addinai da al'adu da tsarin dokoki da gudanar da shari'a da ta haɗar da shari'ar Bature da ta gargajiya da Shari'ar Musulunci.

### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A yaɗa manufa zuwa ga gwamnatocin ƙananan hukumomi da na jahohi da sarakunan gargajiya a kan kawar da ayyuka masu cutarwa da suke shafar mata da 'yammata da masu buƙata ta musamman.
2. A shigar da batun jinsi a manhajar karatu a kowane mataki.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A horar da waɗanda suke aikin 'yansandan al'umma don cikakkiyar fahimta da kula da batutuwan jinsi a matakin unguwa, musamman gudanar da al'adu masu cutarwa.

4. A shigar da batun jinsi a wajen gudanar da kotunan shari'un gargajiya a kuma tabbatar da ba da isasshen horo ga ma'aikatan shari'a.

5. A ƙara ci gaba da ba da horo don a horar da hukumomi kamar ICPC da EFCC da NOA da 'yansanda da jami'an kwastam da ma'aikatan shari'a da jami'an kula da gidajen gyaran hali da NAFDAC da Jami'an Kula da Shige da Fice don su shigar da daidaiton jinsi a tsarinsu.

6. A shigar da ƙa'idodjin GEESI a takardun ba da horo ga cibiyoyin shari'a.

7. A yi aiki tare da masu yin doka don a zartar da Kuduri Dama Bai Ɗaya na 2016 a kuma sa hannu ya zama doka.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.



Ma'aikatar Shari'a a Matakin Tarayya da Jahohi.



Makarantun Koyar da Shari'a.



Ma'aikatun Ilimi na Tarayya da na Jahohi da Hukumar Kula da Jami'o'i ta Kasa da NBTE da sauran hukumomin da samar da manhaja a kowane mataki ya shafa.



Hukumomi da Ma'aikatun Gwamnati kamar ICPC da EFCC da NOA da 'yansanda da jami'an kwastom da ma'aikatan shari'a da jami'an kula da gidajen gyaran hali da NAFDAC da Jami'an Kula da Shige Da Fice.



Sarakunan Gargajiya.

- Masu yaɗa manufa da sauran ƙungiyoyin fararen hula.
- Majalisun Tarayya.

# (B). Hakkin Ɗan'adam da Hakkin Mata

## Halin da ake Ciki:

1. Tsarin Mulkin Nijeriya da Kundin Shari'ar Manya da Kananan Laifuka da gyare-gyare da shari'un gargajiya duk sun daƙile haƙƙoƙin mata.
2. Mata da 'yammata suna ci gaba da fuskantar cin zarafi a wuraren da ya kamata a ɗauka ba su da haɗari.
3. Nijeriya tana fuskantar wasu matsaloli daban, haɗi da kariya daga nuna rashin imani saboda jinsi da kawar da al'adu masu cutarwa da hakƙoƙin renon ciki da goyo da ilimin 'ya'ya mata da shiga cikin ayyukan yanke hukunci.

## Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. Yaɗa manufar amfani da sauran dokokin ƙasa da ƙasa a kan daidaiton jinsi da inganta rayuwar mata da shigar da kowa a zamantakewa (GEESI).
2. A kawar da dukkan ayyukan al'ada da na addini da suke shafar mata da 'yammata.
3. A daidaita batun jinsi a cikin tsarin shari'ar Nijeriya mai fuska uku.
4. A tallafa wa haɗin guiwa tsakanin masu ruwa da tsakin da suka dace a wajen aiwatar da Dokar Jinsi ta Kasa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Hakkin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

5. A riƙa amfani da tsarin kasafin kuɗi da zai tabbatar da adalci da daidaito wajen rabon albarkatu ga mata da maza da 'yammata da yara maza da sauran rukunin marasa galihu a kowane matakin gwamnati da cibiyoyi.

6. A samar da dama bai ɗaya cikin adalci ga mata da maza don su samu su kuma more ayyukan al'umma.

7. A haɓaka dama bai ɗaya cikin adalci ga mata da maza wajen samun jari da aiki da fili da fasaha da dabarun sana'a ta hanyar Shirin Rage Talauci.

8. A ƙarfafa al'adar girmama haƙƙokin ɗan'adam ga mata da maza.

9. A haɓaka ƙarfafa hanyoyin aiwatar da dokokin da suke kula da hukunta ayyukan nuna wariyar jinsi.

10. A haɓaka damar samun ayyukan zamantake wa ga yara da mata da sauran rukunin marasa galihu.

## Masu Ruwa da Tsaki

Ma'aikatar Shari'a ta Tarayya da ta Harkokin Mata.



Majalisun Tarayya.

Kungiyoyin yaɗa manufa da sauran ƙungiyoyin al'umma.



Cibiyoyin addini da na gargajiya.

Gwamnati a kowane mataki.

# (C). Ɗaukar Nauyi da Yin Abu a Buɗe da Shugabanci a Buɗe don Cigaba Mai La'akari da Jinsi

## Halin da ake Ciki:

1. Akwai rashin yin abu a buɗe da rashin ɗaukar nauyi a gwamnati, wanda ya haifar da cin hanci da samar da aiki mara inganci da lalacewar gine-gine da mamaye wasu a siyasa da ma wasu.

2. Tsarin Yaƙar Cin Hanci na Kasa (NACS), wanda aka ƙaddamar a shekara ta 2017 ya gaza wajen samar da tartibiyar hanya ko kai ɗauki.

3. Mummunan jagoranci yana shafar mata da masu buƙata ta musamman da sauran rukunin marasa galihu a Nijeriya.



## Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. Yin Aiki da Fasahar Sadarwa a Nijeriya don a samar da manhajoji a harsunan gida, waɗanda za su magance batutuwan daidaiton jinsi da shigar da kowa a zamantakewa.

2. A haɓaka yin mu'amalar gwamnati a buɗe ta yanar gizo a kuma tabbatar da cewa mata da sauran rukunin marasa galihu suna da damar kai wa ga manyan damammaki.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

3. A gudanar da yaɗa manufa don a ƙarfafa jihohi da yawa su shiga cikin Tsarin Gudanar da Gwamnati a Buɗe.
4. A haɓaka tattaunawa a kai-a kai da muhawara da tattauna batun GEESI a dandalin sada zumunta.
5. A haɓaka samar da alƙaluma a kan jinsi da bayanai a kan maza da mata, waɗanda za a riƙa nazarinsu a ware a rumbun adana bayanai na ƙasa, a kuma tabbatar da amfani da waɗannan bayanan wajen manufofi da tsare-tsaren cigaban ƙasa.
6. A yi amfani da hanyoyin da suka dace don kare mata da 'yammata da sauran rukunin marasa galihu daga cin mutunci da cin zali da kalaman nuna ƙiyayya a yanar gizo.

## Masu Ruwa da Tsaki

1. Gwamnati a kowane mataki.
2. Ma'aikatu da Hukumomin gwamnati haɗi da Ma'aikatar Harkokin Mata da Ma'aikatar Kuɗi da Kasafin Kuɗi da Tsare-tsaren Kasa.
3. Kungiyoyin Yaɗa Manufa da sauran ƙungiyoyin fararen hula.
4. Kamfanonin fasahar sadarwa a Nijeriya.
5. Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA BAKWAI:
# GEESI DA JAGORANCI DA SHIGA SIYASA

## (A). GEESI da Tsarin Siyasar Nijeriya

### Halin da ake Ciki:



1. Wakilcin Mata mara kyau a Majalisun Tarayya - **kaso 4.5 cikin ɗari ne kaɗai.**

2. Jam'iyyun siyasa ba sa ba mata muhimman wuraren shugabanci kuma suna da ƙarancin mayar da hankali ga daidaiton jinsi a wakilcin zaɓe.

3. Yanayin tsari yana kare shigar mata cikin siyasa.

4. Jam'iyyun siyasa ba sa mayar da hankali yadda ya kamata ga ƙa'idojin daidaiton jinsi da inganta rayuwar mata da shigar da kowa cikin zamantakewa (GEESI) a cikin tsare-tsarensu.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A horar da jam'iyyun siyasa su mayar da damuwar mata da maza da 'yammata da yara maza da masu buƙata ta musamman da sauran rukunin marasa galihu a matsayin wani ɓangare na tsarinsu.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*
MacArthur Foundation

2. A tallafa wa yaɗa manufar ƙarin shigar mata harkokin siyasa da wakilci.

3. A tsara ci gaba da faɗakarwa don shiga siyasa da wakilci.

4. A yaɗa manufar dokokin da suka dace da tsarin shari'a don mayar da ƙa'idojin GEESI wani ɓangare na tsarin siyasa na dundundun.

5. A samar da kuɗi don tallafa wa 'yan takara mata a kowane mataki.

6. A tallafa wa ƙungiyoyin al'umma wajen horar da mata a fannin shugabanci a ɓangaren gwamnati da masu zaman kansu.

7. A samar da tallafin kuɗi ko na kayan aiki ga ƙungiyoyi da haɗin kan da zai haɓaka shigar mata harkokin siyasa da wakilci.

8. A nemi tallafin abokan kawo cigaba wajen bunƙasa shigar mata harkokin siyasa da wakilci.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.

Ma'aikatar Harkokin Mata da sauran Hukumomi da Ma'aikatu.



Jam'iyyun siyasa.

Hukumar Zaɓe ta Kasa.



Kungiyoyin yaɗa manufa da sauran ƙungiyoyin al'umma.



Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.

# (B). GEESI da Tsarin Zaɓe

## Halin da ake Ciki:

1. Adadin shigar mata harkokin siyasa na ƙasa shi ne kaso **6.7 cikin ɗari** a kujerun zaɓaɓɓu da na naɗaɗɗu, nesa da adadin duniya na kaso **22.5 cikin ɗari.**

2. Tarnaƙi daban-daban yana kare shigar mata harkokin zaɓe.

3. Hanyoyin gudanar da zaɓe a Nijeriya cike suke da matsalolin da suke yin mummunan tasiri ga shigar mata harkokin siyasa.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A yi amfani da matakan majalisu da na doka da dabaru don a tabbatar da daidaiton jinsi a dukkan kujerun siyasa a rayuwar jama'a.

2. A yi aiki da ƙa'idojin daidaiton jinsi a matsayin wani sharaɗin da Hukumar Zaɓe za ta yi wa jam'iyyu rijista.

3. A samar da tallafin ƙwararru ga jam'iyyun siyasa don shigar da damuwar mata da maza da 'yammata da yara maza da rukunin marasa galihu.

4. A samar da magwajin jinsi don ɗaukar nauyin daidaiton jinsi a dukkan cibiyoyin al'umma.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

5. A haɓaka gwaji na lokaci zuwa lokaci a kan tsari da ayyukan jam'iyyun siyasa don a tabbatar da yin aiki da tsarin daidaiton jinsi da shigar da kowa cikin zamantakewa.

6. A yi wata doka ta aiwatar da Matakin Tabbatar da Kaso 50 Cikin Ɗari a cibiyoyin al'umma.

7. A haɓaka shigar ƙungiyoyin fararen hula a tsarin zaɓe don gwamnati da jam'iyyun siyasa suka riƙa ɗaukar nauyin a kan GEESI.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.

Ma'aikatar Harkokin Mata da sauran Hukumomi da Ma'aikatu.



Jam'iyyun siyasa.



Kungiyoyin yaɗa manufa da sauran ƙungiyoyin fararen hula



Majalisun Tarayya.

Hukumar Zaɓe ta Kasa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# (C). GEESI da Shugabanci a Matakin Unguwa

## Halin da ake Ciki:

1. Tsarin Nijeriya na babakeren maza da juya al'amura da al'adun al'ummomi daban-daban sun hana mata ƙarfin da suke da shi a zamantakewa da siyasa da tattalin arziƙi.
2. Ana yi wa mata tarbiyya a cikin al'ummarsu da su yarda da rashin daidaiton iko, don a fifita maza.
3. Yunƙurin da ƙungiyoyin fararen hula da ƙungoyoyin da ba na gwamnati ba da ƙungiyoyin addini suke yi a cikin al'umma don kawo sauyi a ɓangaren jinsi ya samar da taƙaitacciyar nasara.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A gudanar da yaɗa manufa da shirye-shirye don sauya tsarin da yake ƙarfafa guiwar rashin daidaito da shigar da kowa a zamantakewa a cikin al'ummomi.
2. A haɓaka ilimin manya don maza da mata, a matakin unguwa ta hanyar wayar da kan al'umma da samar da kayan aikin da suka wajaba don shirin.
3. A ci gaba da gudanar da shirin wayar da kai don a dakatar da ɗabi'ar nuna rashin adalci ga masu buƙata ta musamman ta hanyar cewa ba su cancanci wata girmamawa ba.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

4. A gudanar da ba da horo ga ma'aikatan karamar hukuma a kan batun GEESI.
5. A yi haɗin guiwa da sarakuna a matakin unguwanni a kan ba da horo a kan batutuwan GEESI.
6. A tallafa wa Kungiyoyin Fararen Hula da Kungiyoyin da ba na Gwamnati ba, waɗanda suke aiki a matakin unguwa don haɓaka ajandar GEESI.

## Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.

Ma'aikatar Harkokin Mata.

Al'umomin Unguwanni.



Kungiyoyin yaɗa manufa da Kungiyoyin Al'umma da NGO



Sarakunan gargajiya



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# ƁANGAREN DA AKA BA WA MUHIMMANCI NA TAKWAS:
# GEESI DA ƊABI'UN JINSI DA GUDANAR DA AL'ADUN ZAMANTAKEWA

## (A). HAKKOKIN YARA

### Halin da ake Ciki:

1. 'Yammata da yawa, musamman waɗanda suka fito daga gidaje matalauta, har yanzu suna fuskantar wariya.
2. An fi sa 'yammata aikin gida fiye da yara maza, wannan kuwa yana shafar zuwansu makaranta.
3. Tasirin rashin daidaito da mata da 'yammata suke fama da shi yana bayyana ƙarara a lafiyarsu da iliminsu.

### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A gudanar da yaɗa manufa don dakatar da gudanar da al'adu masu cutarwa ga yara mata.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.
MacArthur Foundation

2. A shigo da kasafin kuɗi da zai tabbatar da raba albarkatu cikin adalci ga kowane rukunin jinsi don a nufi buƙatun yara mata, a kowane ɓangare.

3. A tallafa wa samar da gine-gine masu aminci a makarantu da unguwannin don a rage SGBV.

4. A samar shawarwari ga mata da 'yammata da SGBV ya shafa da sauran tashin hankali.

5. A gudanar da gangamin wayar da kai da yaɗa manufa a unguwanni; da shirye-shiryen da suka mayar da hankali ga inganta rayuwar mata ko 'yammata.

6. A haɗa kai da a kuma tallafa wa ƙananan ƙungiyoyin al'umma da da suke aiki a kan haƙƙoƙin 'yammata, musamman ƙungiyoyin mata.

## Masu Ruwa da Tsaki

- Gwamnati a kowane mataki.
- Ma'aikatar Harkokin Mata.
- Shugabannin Addini.



- Iyalai ko Mutanen Unguwa.



- Kungiyoyin Fararen Hula musamman ƙungiyoyin mata.



- Abokan kawo cigaba na ƙasa da ƙasa.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Hakkin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

## (ii). Yaro Namiji

### Halin da ake Ciki:

1. Tsarin zamantakewar da maza su ke riƙe da iko don tauye mata, yana ƙarfafa rashin daidaiton jinsi a Nijeriya, ta yadda ake fifita yaro namiji a kan mace.
2. Karuwar ayyukan ta'addanci da rufe makarantu da yawa a Arewa ya jawo yawan yaran da ba sa zuwa makaranta maza.
3. Hanyar tarbiyyar yara ta gargajiya tana yin mummunan tasiri ga yara maza a kan gina wa kansu kyakkyawan iyali.

### Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A tallafa wa shirye-shiryen da suka nufaci haɓaka shigar yara maza makaranta a Kudu Maso Gabas da Arewa Maso Gabas.
2. A tallafa wa makarantun ilimi su samar da tagomashin da zai haɓaka ilimin yara maza, musamman a Kudu Maso Gabas da Arewa Maso Gabas.
3. A gudanar da yaɗa manufa don yin aiki da kuma aiwatar da Dokar Haƙƙoƙin Yaro a kowace jiha.

4. A samar da gwarzon jinsi da zaman lafiya a tsakanin yaran makaranta maza da mata a kowace jiha a Nijeriya.

5. A samar da yanayi mara haɗari a unguwa don yara maza da 'yammata, waɗanda SGBV ya shafa.

6. A samar da shirin sa wa a hanya ga yara maza da 'yammata a unguwanni; da mayar da hankali ga shirye-shiryen GEESI da nuna damuwa.

## Masu Ruwa da Tsaki

- Gwamnati a kowane mataki.
- Ma'aikatar Harkokin Mata
- Shugabannin Addini



- Iyalai ko Mutanen Unguwa



- Kungiyoyin Fararen Hula
- Sarakuna da shugabannin gargajiya.

# (B). Gudanar da Al'adu Masu Cutarwa

## Halin da ake Ciki:

1. Ana samun gudanar da al'adun nuna wariya ga mata da 'yammata a kai-a kai a kowace ƙabila a Nijeriya.

2. Al'adun tsafi ga waɗanda mazajensu suka mutu suna jefa zawarawa cikin matsanancin halin tattalin arziki da tsarewa da mummunar mu'amala.



3. Ana yawan take haƙƙoƙin yara mata.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A gudanar da yaɗa manufa ga sarakuna da shugabannin gargajiya da na addini a kan daina gudanar da al'adu masu cutar da mata da 'yammata.

2. A sake horarwa a kuma tallafa wa ungozoma, waɗanda aikinsu yi wa mata kaciya, don su sami wasu hanyoyin samun kuɗi.

3. A samu tallafin gidajen yaɗa labarai da dandalin sada zumunta don gangami nuna ƙyamar gudanar da al'adu masu cutar da mata da 'yammata a unguwanni.

4. A tallafa wa tsarin inganta rayuwar tattalin arziki ga mata da masu buƙata ta musamman da zawarawa da sauran rukunin marasa galihu.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki

Ma'aikatar Harkokin Mata.

- Sarakunan gargajiya.
- Shugabannin Addini.
- Ungozomar gargajiya
- Shugabanni ra’ayi.
- Kafafen Sadarwa da dandalin sada zumunta.



Iyalai ko Mutanen Unguwa.



Kungiyoyin yaɗa manufa da sauran ƙungiyoyin fararen hula.

## (C). Nuna Rashin Imani Dangane da Jima'i ko Jinsi

### Halin da ake Ciki:

1. Tsarin al'adun da a tarihance suke nuna wariya ga mata su ne suke da alhakin ɗorewar SGBV.
2. SGBV suna kan ƙaruwa a Nijeriya duk da amincewa da dokar Hana Nuna Rashin Imani ga Mutane (Dokar VAPP) da jahohi 34 suka yi a cikin 36 na ƙasar.
3. Har yanzu ba a zartar da Kudurin JINSI da Ba Da Dama Bai Ɗaya, wanda a hukumance ake kira CEDAW, ba.

### Matakan da ake Buƙatar Ɗauka:

1. A ci gaba da gudanar da faɗakarwa da wayar da kai don a hana tsangwamar waɗanda SGBV ya shafa.
2. A yaɗa manufa zuwa ga sarakuna da masu ruwa da tsaki a unguwa a kan kawar da SGBV ko Nuna wa mata rashin imani (VAW).
3. A samar da isassun kuɗaɗe don tallafa wa waɗanda SGBV ya shafa.
4. A ƙarfafa haɗin kan ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba da abokan kawo cigaba da suke aiki a kan SGBV don kai ɗauki yadda ya kamata.

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.

Ma'aikatar Harkokin Mata.

Kungiyoyin Addini.

Sarakunan gargajiya.



Masu ruwa da tsaki a unguwanni.



Kungiyoyin Fararen Hula da sauran ƙungiyoyin da ba an gwamnati ba.



Abokan kawo cigaba.

# (D). Maza a Cikin Ajandar GEESI

## Halin da ake Ciki:

1. Rashin shigar da maza a dukkan matakai da rashin wayar da kai a tsakanin maza su ne suke jawo jan ƙafa a wajen cimma daidaito tsakanin mata da maza.
2. Maza sun mamaye ɓangaren yanke hukunci da muƙamai a cikin al'umominsu daban-daban.
3. Da alamu maza suna samun ilimi mafi inganci kuma suna sane da batutuwan jinsi amma ana buƙatar ƙarin yunƙuri don a sa maza su bi.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A sami tallafin ra'ayin maza da muhimman shugabanni wajen haɓaka ajandar GEESI.
2. A yi aiki tare da shugabannin gargajiya ko na unguwannin ko na addini ko sauran shugabannin ra'ayi maza wajen samar da ajandar GEESI a unguwannin.
3. A gudanar da horo a kan jinsi ga maza da muhimman shugabanni.
4. A gano a kuma yi aiki tare da gwarazon maza a matsayin muhimman shugabanni a wajen haɓaka ajandar GEESI a unguwanni.
5. A riƙa girmamawa a bainar jama'a, a kuma riƙa amince wa mazan da suke magana don mata.



Samarwa daga
Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA

Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.

MacArthur Foundation

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki.

Ma'aikatar Harkokin Mata.

Sarakunan gargajiya.

Shugabannin Addini.



Mutanen Unguwa.



Kungiyoyin fararen hula da ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba, waɗanda maza ke jagoranta.



Shugabannin Ra'ayi Maza.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# (E). Sauya Mulkin Kananan Hukumomi

## Halin da ake Ciki:

1. Hanyoyin kai ɗauki don tallafa wa GEESI a matakin unguwanni da cibiyoyi ba su da inganci.
2. Kai ɗauki a mataki ƙaramar hukuma, don hana afkuwar Nuna rashin imani dangane da jima'i ko jinsi ga mata da 'yammata, ba shi da inganci.
3. Ana jan ƙafa wajen magance batutuwan kaƙƙoƙin mata da na shigar da kowa cikin zamantakewa a matakin ƙaramar hukuma.

## Matakan da ake Buƙatar Dauka:

1. A nemi tallafin Kungiyoyin Al'umma da abokan kawo cigaba don su samar wa da shirye-shiryen GEESI kuɗi a matakin ƙaramar hukuma.
2. A tallafa wa ƙungiyoyin Al'umma su shiga cikin shirye-shiryen inganta rayuwar tattalin arziki don mata da sauran rukunin marasa galihu.
3. A samar da horon shugabanci ga mata tun daga tushe don a ba su dama su shiga cikin jagorancin al'umma da siyasa.
4. A gudanar da gangamin nuna ƙyama ga gudanar da al'adu masu cutarwa da suka saɓa wa ƙa'idodjin GEESI a unguwanni.
5. A yi aiki tare da masu riƙe da sarautun gargajiya da shugabannin addini a unguwanni don tallafa wa ajandar GEESI.



*Samarwa daga*
*Kungiyar Kare Haƙƙin Mata WRAPA*

*Tallafi daga Gidauniyar MacArthur.*

MacArthur Foundation

# Masu Ruwa da Tsaki

Gwamnati a kowane mataki, musamman ƙaramar hukuma.

Ma'aikatar Harkokin Mata.

- Sarakunan gargajiya.
- Shugabannin Addini.



Kungiyoyin A'umma.



Kungiyoyin fararen hula na gida da na ƙasashen waje.



Kungiyoyin Yaɗa manufa.

**Youtube:**
WRAPA Nigeria

**Facebook :**
WRAPA Nigeria

**Twitter :**
@wrapang

**Imel:**
Info@wrapanigeria.org and
wrapa399@gmail.com

**Adreshi:**
A.E. Ekukinam St, Utako 900108, Abuja,
Federal Capital Territory

**Lambar Waya:**
07063807887; 08172125692;
0804 0006176 - (Direct line to Legal Unit)

**Shafin Yanar Gizo:**
www.wrapanigeria.org

**Instagram :**
@wrapang